# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Kowa dabam Allah ya yi shi: Mutunta haƙƙin tsirarru
## Kashi na uku: ’Yan Zimbabwe da ke yaƙar ƙyama ga masu ƙwayar cutar HIV

| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | Columbus Mavhunga |
| Wanda ya fassara: | Ɗanlami Bala Gwammaja |
| Wadda ta tace: | Halima C. Schmaling |


**’Yan Wasa:**

Mai ba da labari

| | |
|---|---|
| Brian: | ɗan shekara 23 |
| Alex: | ɗan shekara 21 |
| Chengetai Dziwa: | ɗa namiji |
| Dr Nzika Mahachi: | ɗa namiji |
| Johannes: | ɗan shekara 29 |
| Rue: | ’yar shekara 22 |

**Mai gabatarwa:**

Jama'a, barkanmu da sake kasancewa da ku a cikin shirinmu na "Ji Ka Karu" kashi na uku mai suna "Kowa Dabam Allah Ya Yi Shi – Mutunta Haƙƙin Tsirarru". A cikin wannan kashi na uku na wannan shirin za mu gana ne da waɗansu matasa ne 'yan Afirka a kan yadda al'amarin masu fama da cutar HIV ya zama abin magana a nahiyar, sun kuma faɗa mana yadda abin ya shafe su. Sai ku biyo mu, mu rankaya zuwa ƙasar Zimbabwe, wato ɗaya daga cikin ƙasahen da suke da waɗanda suka kamu da wannan cuta masu yawa a nahiyar Afirka.

**Mai ba da labari:**

Waɗannan matasa ne da suke ɗauke da ƙwayar cutar HIV. Suna haɗuwa a kowace ranar Asabar da rana a tsakiyar Harare, babban birnin ƙasar Zimbabwe, don su tattauna halin da suke ciki. A cikinsu akwai wani matashi ɗan shekara 23 da za mu kira Brian. Ya ce an haife shi ne da wannan ƙwayar cuta. Iyayensa duka biyu ma sun yi fama da wannan cuta. Ya yi bayani cewa abu ne mai wahala gare shi ya iya jure bambancin da ake nuna masa lokacin da aka gano yana ɗauke da ƙwayar wannan cuta yana ɗan shekara goma kacal.

**Bayanin Brain cikin Turanci:**

*"Lokacin da na fahimci ina ɗauke da wannan ƙwayar cuta, sai duk na tsani kaina. Haka kuma na fuskanci wannan matsalar ma daga waɗansu, har ma a makaranta. Irin maganganun da suke faɗa mini da irin wasan da suke yi ba daɗi. Ba wai wani suna suka saka mini ba, amma irin maganganun da suke faɗa su ne: "Me ya sa leɓenka yake yin ja?", ko "Me ya sa kake yawan rashin lafiya?", "Kai ke nan yau da lafiya gobe babu".*

**Mai ba da labari:**

A halin yanzu Brian ya koyi jure wa irin wannan bambancin da ake nuna masa. Yakan ce: "Abin ya daina damuna."

**Bayanin Brain cikin Turanci:**

*"Da farko dai sai na rungumi ƙaddara. Ba yadda na iya. Rungumar ƙaddara shi ne maganin da na fara amfani da shi. Na biyu kuma ba na wasa da maganin da likitoci suke rubuta mini. Abu mafi muhimmanci gare mu, mu masu ɗauke da wannan ƙwayar cuta, shi ne shan wannan magani kamar yadda yake a ka'ida."*

**Mai ba da labari:**

Shi kansa Brian a yanzu idan yana bayani kai ka ce likita ne ko wani mai bayar da shawarwari. Ya kuma faɗi gaskiya da ya ce: samun kulawar likitoci tana da muhimmanci. Shan magani a kai-a kai yana taimakawa wajen daƙile ƙarfin wannan kwayar cuta ta HIV. Nan tsallaken gari ga gidan "Zvandiri nan", wato ofishin ƙungiyar ta "Afric Aid".

Wannan ƙungiya ce da take hurɗa da matasa masu ɗauke da ƙwayar HIV. *Zvandiri* wata kalma ce ta harshen Shona mai nufin "yadda nake". Matasan da suke ɗauke da wannan ƙwayar cuta ta HIV ne suka fito da ita, wato suna cewa, "ku zauna da mu yadda muke". An gano Alex yana ɗauke da wannan ƙwayar cuta a shekara ta 2007 lokacin yana ɗan shekara 16. A halin yanzu yana aikin sa-kai ne mai bayar da shawarwari. Alex cewa ya yi, ya kamata duk matasan Zimbabwe su je a gwada su don su san matsayinsu. Da aka tambaye shi dalili sai ya yi murmushi ya ce.

**Bayanin Alex cikin Turanci:**

*"Na samu nutsuwa lokacin da na san matsayina. Ka huta da yawan tunani, kamar: me ya sa nake yawan rashin lafiya, me ya sa ban je makaranta ba? Amma idan ka san matsayinka, to za ka samu nutsuwa da yanayin da ka samu kanka a ciki. Kuma ba ni da wata damuwa a kan halin da nake ciki. Na rungumi ƙaddara, kuma hannu bibbiyu."*

**Mai ba da labari:**

Burin Alex shi ne ya zama ma'aikacin jiyya don ya ji daɗin taimaka wa matasan Zimbabwe su yaƙi cutar HIV. Amma fa ba wannan ne kaɗai burin nasa ba.

**Bayanin Alex cikin Turanci:**

*"Ina son na yi aure na haifi ’ya’ya waɗanda ba su da ƙwayar cutar HIV. Ko da nan da shekara biyar ma. A halin yanzu ina da budurwa. Ina sonta sosai. Sai dai mukan fuskanci matsaloli kamar kowa, amma dai muna tare."*

**Mai ba da labari:**

Ba Alex da Brian ba ne kawai matasan da suke ɗauke da ƙwayar cutar HIV suke gudanar da rayuwa ba tare da wata damuwa ba. Amma a wurin waɗansu abin da kamar wuya.

**Bayanin Rue cikin Turanci:**

*"Yayin da aka yi gwajin babata kasa faɗa mini sakamakon ta yi, sai bayan shekara biyar. Wannan bai dace ba. Ba mamaki tana da dalilin yin haka. Daga nan fa sai na dinga fuskantar ƙyama, har ma daga mutanen gidanmu.*

**Mai ba da labari:**

Bari kuma mu kira wannan budurwa ’yar shekara 22, Rue. A halin yanzu tana aikin sa-kai ne na mai bayar da shawara a ƙungiyar Afric Aid kamar dai Alex. Ta yi bayanin cewa, ɗan’uwanta ya hana ta zaɓi irin karatun da take son yi. Bagu da ƙari lokacin da aka gano tana ɗauke da ƙwayar cutar HIV, sai ya zamana ɗan’unwan nata ne yake yanke hukunci a kan duk wani abu da za ta yi, shi ne kuma yake zaɓar mata ƙawaye, kai har ma lokacin da za ta kwanta shi ne yake zaɓar mata.

**Bayanin Rue cikin Turanci:**

*“Irin waɗannan ƙalubalen ne suka shafi irin aikin da na samu kaina a ciki. Daga ƙarshe dai na yanke shawarar yin aikin jiyya. Amma samun damar yin wannan aikin ma da ƙyar ta yiwu saboda ganin irin halin da muke ciki. Muna dai fuskanta ƙalubale iri-iri."*

**Mai ba da labari:**

A yanzu ta yi bayanin cewa, wannan ɗan’uwan nata ya yi hakan ne a bisa

rashin sani.

**Bayanin Rue cikin Turanci:**

*"Yanzu na daina damuwa da ƙyamar da ake nuna mini. Watakila ɗan'uwana bai fahimci halin da nake ciki ba. Shi ya ɗauka abin da ya dinga yi mini ɗin nan shi ne ya fi dacewa, bayan kuma ba haka ba ne. Saboda rashin lafiyar da na dinga fama da ita sai duk ya ƙosa, yake ganin hankalin kowa a gidan yana kaina. Sai yanzu na fahimci dalilin abin da ya faru. Ko da yaushe sai faman faɗa muke ta yi da shi."*

**Mai ba da labari:**

Burin Rue shi ne a samu zaman lafiya tsakanin mutanen ƙasar Zimbabwe, tana kuma fatan irin wannan yanayin ya wanzu har a tsakanin mutanen gidansu. A halin yanzu tana ta ɗokin zuwan lokacin da za a yi bikinta a watan Afrilu. Wanda zai aure ta tuni ya biya iyayenta kuɗin sadaki don a samu a yi bikin. A al'adar ƙasa ta Zimbabwe sadaki ya ƙunshi kuɗi ne da kuma shanu kimanin guda goma. Shi wanda zai aure ta ɗin wanda shekara uku ke nan da sa ranar ba shi da ƙwayar HIV a jininsa. Rue ta yi bayanin irin maganganun da iyayenta suka yi yayin da suka ji labarin shirye-shiryen auren.

**Bayanin Rue cikin Turanci:**

*"Sun yi mamaki, saboda kusan ba wanda ya zaci abin. Amma sun taya ni murnar saboda suna ganin na yi abin da ya dace."*

**Mai ba da labari:**

Shi wanda zai auri Rue ɗan kasuwa ne kuma shekarunsa 29, a kuma Harare yake da zama. Da ƙyar ya yarda ya tattauna da mu a kan wannan batu, amma ya yi alƙawarin ganawa da mu bayan ya tashi daga aiki. Yayin da muka isa gidansa dare ya yi. Ba wuta, sai ƙarar janareto kawai kake ji daga 'yan gidajen da suke da su.

Daga nan sai muka shiga mota muka je wata mashaya da take nan kusa inda mutane ke kallon bal suna kuma sauraron kiɗa. Sai muka zauna a mota don mu ji bayanin Johannes, wato wanda zai auri Rue. Da farko dai Johannes ba a

nutse yake ba. Sai muka buɗe *window* muna sauraron kiɗan da yake tashi daga wannan mashaya. Daga baya kuma sai Johannes ya fara bayani.

**Bayanin Johannes cikin Turanci da Shona:**

*"Ba na son na jefa kaina cikin matsi. Ina son na zauna rayuwata ta zama mai sauƙi. Wannan ita ce magana. Tunanin da na yi shi ne: idan na guji Rue, to ina za ni? Abu ɗaya tak ya dame ni, har yanzu yana ƙara damuna. Ta yaya zan samu ɗa. Amma duk da haka za mu yi aure mu kuma zauna har ta Allah ta kasance."*

**Mai ba da labari:**

Johannes ya ce, har yanzu bai faɗa wa iyayensa cewa wadda zai aura tana ɗauke da ƙwayar cutar HIV ba. Yana jin ba za su yarda matar da zai aure ta zama tana ɗauke da wannan cuta ba. Ɗaya daga cikin tunanin da ake yi wa masu ɗauke da ƙwayar cutar HIV shi ne, ba za su haifi 'ya'ya waɗanda ba su da wannan ƙwayar cutar ba. Ba laifi idan aka yi musu wannan tunanin, amma fa ba shi da tushe. Yawanci tana iya yiwuwa iyayen da ɗaya daga cikinsu ne yake da wannan ƙwayar cuta su haifi ɗa wanda ba shi da ita. Hakan zai yiwu ne ta hanyar samu kulawar likita.

**Bayanin Nyika Mahachi:**

*"A wannan matakin muna da ƙwaƙƙwarar shaidar cewa, shan maganin dakushe kaifin wannan cuta yana da muhimmanci wajen kare ɗaya daga cikin ma'auratan da ɗayansu yake ɗauke da wannan ƙwayar cuta ta HIV. Don haka idan ɗaya daga cikinsu yana ɗauke da wannan ƙwayar cuta, kuma yana shan maganin, sannan kuma aka dace maganin yana tasiri a kan ƙwayar cutar, to suna iya sa ran haifar ɗan da ba shi da ita. An gano wannan ne ta hanyar da ake kira da "viral load", wato ƙarfin ƙwayar cutar, da kuma "CD4 count".*

**Mai gabatarwa:**

Da wannan muka kawo ƙarshen wannan kashi daga cikin shirye-shiryenmu na "Ji Ka Karu" inda aka yi bayani a kan yaƙi da nuna ƙyama ga masu ɗauke

da ƙwayar cutar HIV a Afirka. Columbus Mavhunga ya kawo mana wannan rahoton daga ƙasar Zimbabwe.

Idan kuna muradin sake sauraron wannan shirin za ku iya samun shirye-shiryenmu na "Ji Ka Karu" a adireshinmu na yanar gizo, wato dw.de/lbe. Kuna kuma iya aiko mana su ta shafinmu na 'Facebook'.